Manzon Allah SAW ya shafi Hannunsa a fuskarsa kuma yayi mun Addu'a , sai ya rayu shekara xari da Ashirin kuma babu komai a kansa sai 'Yan gasuka kaxan farare

Daga Abu Zaid Bn Akhxab -Allah ya yarda da shi- ya ce: "Manzon Allah SAW ya shafi Hannunsa a fuskarsa kuma yayi mun Addu'a , sai ya rayu shekara xari da Ashirin kuma babu komai a kansa sai 'Yan gasuka kaxan farare"

[Ingantacce ne] [Al-Tirmithi Ya Rawaito shi - Ahmad ne ya rawaito shi]

Manzon Allah SAW ya shafa hannunsa akan fuskar Abu zaid Bn Akhxab Al-ansari -Allah ya yarda da shi- kuma yayi Masa Addua a wata riwayar kuma ta hadisin cewa shi yayi masa Addu'a da wannan Addu'ar "Allah ka ka Qawata shi, kuma ka tabbatar da Kyawunsa" ai ka sanya shi kyakkyawa Kuma ka Sanya Kyawunsa Dawwamamme tare da shi tsawo rayuwarsa, Azara xaya daga cikin waxanda suka rawaito Hadisin yana cewa: lallai Abu Zaid Al-ansari ya rayu shekara Xari da Ashirin kuma babu Furfura akansa sa yan silalan gashi farare, kuma a cikin wata riwayar: cewa shi ya kasance ne Mai sakin Fuska kuma bashi da Mokaxar fata ko kuma nannaxewa, kuma haka ya zauna har ya Mutu, kuma wannan duk saboda Al-barkar Addu'ar Manzon Allah SAW da kuma Shafar da yayi Masa a Fuskarsa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/10955